International Journal of Innovative Language, Literature & Art Studies 11(4):7-13, Oct.-Dec., 2023
© SEAHI PUBLICATIONS, 2023 www.seahipaj.org ISSN: 2467-8511

Tasirin Zamananci Kan Sunayen Yanka Na Karai-Karai A Yau

ISHAKU Abubakar

Department of Hausa,
Umar Suleiman College of Education Gashu'a, Yobe State, Nigeria
Correspondence E-mail: ishakucity4@gmail.com
(08066735158, 08025096644)

ABSTRACT
As the name implies, Tasirin Zamananci kan sunayen yanka na Karai-Karai a yau" The paper pointed out the influence of contemporary name on Karai-Karai personal names. The users of such names were the Karai-Karai especially youths (male and female) who get into new marriage life, whose ages ranges from 25-50 years old. Among the names include, Mujahid, Muhibbat, Sabir, Walid, Walida, Sukura, Haidar, Ummi, Hafiza, Anas, Hanif, Khalifa, Momi etc.Twenty respondents were chosen from the target population. Unstructured interview, special observation and library works were employed as a means of data collection. The paper also adopted Ado. A. (2019:89) Diffusion theory of cultural Spread - ra'in Bazuwar al'adu. Additionally, watching television stations such as Tauraruwa, Canal Hausa, Arewa 24, Hijra, Hausa 7, My Hausa Movie, Farin Wata etc, readings of Hausa love books, interactions, travelling etc are responsible factors for the change of name. Finally, the research revealed that there is strong usage of contemporary names by Karai-Karai youths (male and female) especially those that get into new marriage life (new parent).
Keywords: tasiri, zamani, Karai-Karai, Sabir, matasa.

GABATARWA

Harshen Karai-Karai na ɗaya daga cikin harsunan Arewa maso gabashin Nijeriya, ana samun sa a Jihar Borno da Yobe da Bauchi. A Jihar Yobe, za a same shi a Yobe ta Kudu (Yobe South Senatorial District) wato a Karamar Hukumar Fika da Fune da Nangere da Potiskum inda ya yi maƙwabtaka da al'ummar Ngizimawa da Bolewa da Ngamawa da Fulani da Kanuri (Abubakar, 2022:Sh. 231-237). Baya da haka, harshen ya kasance ɗaya daga cikin harsunan Iyalan Chadi, ɓangaren Yamma rukunin A (West A) yankin ɓangaren harsunan Afirka da Asiya – Afro-Asiatic (Greenberg, 1963: Sh. 647). Bugu da ƙari, sannan, ɗaya daga cikin harsuna bakwai na Iyalan Chadi da suka kasance 'yan asalin Jihar Yobe, sauran sun Bade da Ɗuwai da Ngamo da Ngizim da Bole da sauransu (Newman, 1977, Sh. 77). Duba ga bayanin shehin malami, harsuna iyalan Chadi, suna da yawa, amma harshen Ngamo da Bole da Ngizim da Karai-Karai da Bade da Duwai da sauransu sun faxo qarqashin Jihar Yobe Greeenberg, (1950, Sh. 647, 1966, Sh. 44-47) yana da wannan fahimta.

Karai-Karai, al'umma ce da take da majiya da yawa wadda ya haɗa da Musulmai da Kiristoci. Sannan, a da ta kasance tana amfani da sunan gargajiya a matsayin sunan yanka kafin zuwan Addinin Musulunci da Kiristaniti. Sai dai, bayan zuwan Addinin Musulunci da Kiristanici sai tsarin sunan yanka ya sauya inda ya koma irin na Addinin Musulunci da Kiristaniti kamar Philip da Solomon da Simon da Ehud da Rebecca da Gloria da Muhammad da Musa da Ibrahim da Yusuf da Aisha da Khadija da sauransu (Abubakar, 2022: Sh. 231-237).

Sunan zamani, suna ne da zamani ya kawo wadda kuma ke ƙoƙarin zama ruwan dare a tsakanin al'ummar Karai-Karai musamman sababbin iyaye – iyaye sabon shiga musamman matasa (maza da mata) na

wannan zamani waɗanda shekarunsu ya fara daga ashirin da biyar zuwa hamsin da haihuwa. Ado, (2012: Sh.24-51) ya nuna cewa sunan gargajiya suna ne da aka gwama shi da na zamani. Suna kalma ce da ake amfani da ita don ambaton wani abu ko wajen kiran wani abu (Danmaigoro, 2010: sh. 158-168), sunan yanka kuwa, suna ne na ainihi kuma zahiri wanda kowa da kowa ya amince (Gwammaja, 2013: Sh.8-9). Saboda haka, wannan takarda za ta bi sawun hanyoyin da suke samar da irin waɗannan sunayen tare da dalilan da suka sa ake amfani da sunayen kana da tasirantuwarsa a tsakanin sababbin iyaye/sabon shiga iyaye musamman matasa (maza da mata) kamar yadda bincike na sarari ya nunar, akasari matasa su suka fi amfani da sunayen. Daga ƙarshe, wannan takarda za ta fito da nau'o'in sunayen tare da shawarwari kan yadda za a rage ko magance matsalar. Irin waɗanan sunaye a zahiri mutum zai iya cewa sunan laƙabi ne, amma idan aka sake duba wa, za a ga cewa ya bambanta da sunan laƙabi, domin sunan laƙabi na amfani da sunan rana wadda kan tsaya a madadin sunan yanka, Ga ma abin da Abubakar, (2001: Sh.30) ke cewa:

> "Hausawa na sanya wa 'ya 'yansu sunan laƙabi ta hanyar la'akari da ranar da aka haifi yaro ko yarinya. Misali. Wadda aka haifa ranar juma'a ana kiranta da jummai, wadda aka haifa ranar laraba ana kiranta da Larai, wadda aka haifa ranar asabar ana kiranta da Asabe. Haka nan, wadda aka haifa ranar lahadi ana kiranta da ladi da sauransu."

Duba ga bayanin malamin, za a fahimci cewa sunan laƙabi suna ne da ake sanya wa yaro ko yarinya ta hanyar amfani da sunan rana, kamar yadda aka nuna, saɓanin sunan zamani wanda ba ya la'akari da lokaci da rana da yanayi da surar jariri ko jaririya.

Kodayake, sanya irin waɗannan sunaye ba sabon abu ba ne, domin hakan ya faru da wasu al'ummu a wasu wurare kamar yadda za a gani nan gaba, wadda al'ummar Karai-Karai ba ta kasance bare ba. Hanzari a nan, shi ne idan ba a ɗauki matakai da suka dace ba, za a wayi gari babu Hamza babu goɗiyar Hamza. Ma'ana babu sunan gargajiyar da sunan yanka ga al'ummar Karai-Karai sai sunan zamani wadda wannan wata hanya ce ta vacewa ko mutuwar harshe, wanda masana da manazarta da ɗaliban harsuna ke kira da babbar murya ta hanyar rubuce-rubuce da tarukan qarawa juna sani tare da faɗakarwa da shawarwari kan yadda za a kare tare da ceto harshen da ya faxa tekun mamaya ko vacewa (Abubakar,2018).

Duba ga matasa su ne manyan gobe, sai ka ga yaro ko yarinya misali sunansa Musa amma ana kiransa da Anas ko Aisha ana kiranta da Siyama. Haka nan, Ibrahim ana kiransa da Khalifa. Kazalika Adama ana kiranta da Sukura. Haka kuwa Aliyu, ana kiransa da Haidar. Garba ana kiransa da Khalil da sauransu. Wata ma sunan Adama ce amma yanzu sunan ya koma gaba ɗaya Hamra gida da waje sakamakon sunan ba shi da dadin ji a kunne (Hira da wani uba). Wanda duk waɗannan ba sunayen Karai-Karai ba ne na yanka ko na gargajiya ba.

Madauci da wasu (1982: Sh. 6-9) cewa ya yi, a al'adar Bahaushe, ana raxa wa yaro ko yarinya suna bayan sati xaya da haihuwa. Sannan sukan kasance daga cikin sunayen Annabawa guda ashirin da biyar. Baya ga haka, sunayen suna da kwatankwacinsu na gargajiya, kamar Adam ana kiransa da Ado, Muhammadu kuwa ana kiransa da Inuwa, Ibrahim ana kiransa da Iro da sauransu. Saboda haka, wannan ya nuna cewa daman ana raxa wa yaro ko yarinya suna. Sai dai wannan xin ya kasance kutse ne zamani inda ake samun wasu suke aron wasu sunaye suna raxa wa 'ya'yansu savanin na al'adarsu.

Shi kuwa Bunza (2012: Sh. 651-659) cewa ya yi "Da yawa sunayen yanka da ake sa wa matan Hausawa a wannan zamani sun kasance ana sanya su ne ba tare da waiwayen tarihin mai sunan na asali ba, balle a yi tunanin neman tubarruka ga wanda aka sanya wa sunan". Haka nan, Sallau, (2011: Sh. 126-130) ya ce Hausawa na raxawa 'ya'yan da suka haifa suna ta hanyar yanayi da rana da lokaci.

Duba ga bayanin Bunza (2012), za a fahimci cewa, abin yana ƙoƙarin zama ruwan dare wanda Hausawa ke masa kirari da 'game duniya' Har wa yau, Babalala, (2022) a rahotan da ya gabatar, ya nuna cewa a Kamaru, zamananci na ƙoƙarin shafe al'adar ƙabilar Lar kuluku ko kiɗar.

Akasarin al'umma, musamman matasa (maza da mata) suna sanya wa 'ya 'yansu irin waɗannan sunaye, kamar yadda aka nunar a baya, ba tare da sanin ma'ana ko tarihin mai sunan ba, balle a nemi albarkar sunan (Hira da wasu iyaye). Don Karin bayani duba Bunza, (2012). Kamar yadda aka nuna a sama, wannan matsala ba ta taƙaita ga al'ummar Karai-Karai ba, haka yake ga al'ummar Hausawa (Bunza,2012) da ma sauran al'ummu, kamar qabilat Lar Kuluku ko Kidar (Babalala, 2022) da sauransu.

Sananne ne cewa, iyaye a zamanin da suna sa wa ‘ya‘yansu sunaye ta hanyar takwara da manufar ya gaji mai sunansa wajen hali mai kyau ko ilmi ko haƙuri ko kyauta da makamantansu, saɓanin a yau kamar yadda tarihin baka (Oral tradition) ya nuna.. Da yawa daga cikin iyaye suna sanya wa ‘ya ‘yansu suna ba tare da sanin ma’ana ko muhimmancin yin haka ba. Kodayake, kowanne zamani da irin nasa salon, amma dai ya bambanta da irin wannan.

Matsalar Bincike

Babu shakka duk wani bincike da aka gudanar yana da matsala da ta haddasa gudanar da binciken. Matsalar wannan bincike ita ce yawaitar sunayen zamani a tsakanin iyayen yau na zamani (iyaye sabon shiga) Karai-Karai musamman matasa (maza da mata) suke sanya wa ‘ya ‘yansu wadda sannu a hankali yake ƙoƙarin shafe sunan yanka da aka raɗa wa yaro ko yarinya.

Manufar Bincike

Hausawa na cewa “Gyara kayan ka bai zamo sauke mu raba ba” Abin nufi shi ne manufar wannan takarda ita ce jawo hankali tare da faɗakarwa ga al’ummar Karai-Karai, musamman shugabanni da masu ruwa da tsaki a cikinsu, manya da qanana, maza da mata kan kada a yi masu sakiyar da babu ruwa. Ma’ana ana faxakar da su don su lura a kan matsalar vacewar sunayensu na yanka da na gargajiya kada a wayi gari babu sunan gargajiya balle na yanka ga ‘ya ‘yansu, a cikin al’ummarsu.

Muhimmancin Bincike

Wannan bincike yana da matuƙar muhimmanci ga al’ummar Karai-Karai musamman shugabanni da masu ruwa da tsaki da sauran jama’arsu. Maza da mata, babba da yaro da tsofaffin cikinsu. kamar haka:

Da farko, bincike zai faɗakar tare da jan hankali kan kutsen zamani a cikin al’adar raxa wa ‘ya’yansu sunaye na yanka da kuma laqabin gargajiya a tsakaninsu kan sunayen ‘ya ‘yansu na yanka. Haka kuma, takarda za ta faxawa al’ummar Karai-Karai barazanar da zamani ke yi mata wajen adana harshensu ta vangaren sunayen yanka da na gargajiya na ‘ya’yansu.

Sannan gudumawa ce a fagen ilmi.

Iyakar Bincike

Wannan bincike ya keɓanta ga sababbin iyaye Karai-Karai (maza da mata) waxanda suke gaban shiga harkar raxin suna, musamman matasa da ke Karamar Hukumar Fika da Nangere da Potiskum. Haka kuma wata farfajiya ita ce ta al’adar raxin suna. Abin nufi, ta taqaita a kan yadda ake raxin suna a yau, a wannan zamani na Karni 21.

Nau’in Bincike

Nau’in wannan bincike shi ne bincike na hali da ake ciki wato shiri kan gama-duniya inda ake samun sauye-sauyen abubuwa da yawa waxanda sakamakon haka sai a rasa ido garin gyaran gira. Ma’ana sai a rasa al’amura na asali ko gargajiya sakamakon zamananci wanda bai taqaita ga al’ummar Karai-Karai ba har sunan yanka na diyan matan Hausawa da qabilar Lar Kuluku. Don Karin bayani Duba Bunza, (2012) da Babalala, (2022).

Hanyoyin Tattara Bayanai

An bi hanyoyi guda uku a wajen tattaro bayanai da ke cikin wannan takarda, kamar lura na musamman (special observation) da hira ko tattaunawa da sabbabin iyaye (sabon-shiga rayuwa ta zama iyaye) kan raxin suna, (maza da mata) musamman matasa waɗanda shekarunsu ya fara daga ashirin da biyar zuwa hamsin da haihuwa. Sannan, an yi amfani da mutane ashirin; Biyar daga Karamar Hukumar Fika, biyar daga Karamar Hukumar Nangere, sannan goma daga Karamar Hukumar Potiskum. Baya da haka, an yi amfani da rubuce-rubucen masana da manazarta da suka gabata.

Ra’in Bincike

Wannan takarda ta yi amfani da Ado, A. (2019:89) ra’in bazuwar al’adu – Diffision Theory of Cultural Spread. Wannan ra’i yana magana a kan cewa, mutane ko al’adun wasu mutane sukan bazu zuwa cikin wasu al’uumu da yawa a cikin duniya. Ma’ana mutane sakamakon qaura da tafiye-tafiye kan tashi daga mazauninsu zuwa wasu wurare, a wannan hali, sai a ari wasu al’adu na daban. Wannan ra’i ya samu karvuwa da fahimtar masana da manazarta kamar (Gusau, 2015: Sh.42; Danmaigoro, 2014: Sh.258) da sauransu. Al’ummar Karai-Karai musamman sababbin shiga iyaye matasa (maza da mata) sun karɓi wannan al’ada hannu bibiyu a matsayin zamananci. Ke nan, ya dace a yi amfani da wannan ra’i a wannan bincike.

Sauye-Sauyen Raxin Suna

Nau'o'in sunaye waxanda ke shafar al'ummar Karai-Karai sun hadà da na Larabci da Turanci da sauransu. Kodayake, a wannan bincike, sunayen Larabci sun fi yawa. Daga ciki akwai Khalil da Sahib da Ajmal da Khalifa da Muhibbat da Mufida da Siyama da Ɗahira da Sabira da Sabir da Walida da Walid da Adnan da Afnan da Hafiza da Ilham da Hanif da Sukura da Sarad da Subwan da Abba Khalil da Lawiza da Hamra da Ummi Salma da Uzaifa. Sai kuma na Turanci kamar anti da barista da sauransu. Duk wadànnan sunaye da aka kawo da ma wadànda ba a kawo ba, ba sunayen Karai-Karai na yanka ko na gargajiya ba, sannan, sunayen sun zo ne a bayan sunan yanka. Ke nan, idan ba a kawo ɗòki ba, lallai, sannu a hankali za a wayi gari duk sunayen Karai-Karai na yanka sun shiga garari.

Hanyoyin da suke kawo Sauyin Raxin sunayen zamani

Akwai hanyoyi da yawa da sababbin iyaye suke amfani da su wajen sanya wa 'ya 'yansu irin wadànnan sunaye. Daga ciki akwai:-

Kallace-kallacen wasu Na'urorin Zamani:

Wannan yana da nasaba da kallon tashoshin talabijin kamar Arewa 24 da Farin Wata da Hijra da Hausa 7 da Tauraruwa da Islamic Library TV da My Hausa da Canal Hausa da Tambarin Hausa da ma fina-finan Hausa. Wasu iyaye suna kallon waxannan tashoshin talabijin a gidajensu ko makwabta. Wasu kuma, sukan sanya kallace-kallacen a wayoyinsu na hannu wadda a ke kira da Turanci 'Handset'. Ana iya kallo ta manhajar sada zumunta ta 'whatsapp' da 'You tube' da 'Istagiram' da 'facebook'. Wasu kuwa, saukewa suke yi a kan wayoyin kai tsaye. Bincike ya nunar, kaso casa'in da tara da ɗìgo biyar na fina-finan Hausa duk an gina su a kan soyayya ce. Saboda haka, a nan, wasu sababbin iyaye suke samun sababbin sunayen, har su raxa wa yaransu. A wannan bincike, wannan kafa ta ɗauki kaso mai yawa wajen samar da sunayen zamani. Baya da haka, wannan kallo bai taƙaaita ga birane ba, har ƙauyuka. A yau, xaixaikun ƙauyuka ne da ba su da gidajen bidiyo, sannan idan ma ta kasance ba su da gidan bidiyon, ana tura masu fina-finan a wayoyinsu na hannu. Akwai na kyauta da ake turawa tsakanin mutum da mutum, akwai kuma na kasuwanci, inda za ka biya kudì a tura maka ko guda nawa kake so. (Hira da wasu iyaye).

Cudànya da wasu harsuna ko mutane:

Wannan ita ma wata hanya ce da wasu sabon shiga iyaye suke amfani da ita wajen samun sunaye da suke raxa wa 'ya'yansu sunan zamani. A nan, zamantakewa tsakanin al'ummu ko harsuna daban-daban kan sa a yi aron wasu abubuwa da yawa. Ba lallai aron sunayen sunan zamani ba, zama irin na cikin unguwa ko ƙauye da makamantansu, kan sanya a yi cuxanya da baqi, har a yi aron al'adun juna.

Rediyo:

Wannan ita ma wata kafa ce ta sadarwa ko isar da wani saƙo. A wannan hali, akwai rubutattun wasan kwaikwayo wadànda aka mayar da su fim ko fina-finai na Hausa da makamantansu waxanda ake sanya wa a ji su da kunne. Wasu kuma, a karanta a gidajen rediyo da tashoshin FM, don sauraro. Sannan sauraron ya danganci ƙarfi ko girman gidan rediyon, inda za a iya kamawa a saurara sosai. Misali, gidan rediyon Kaduna da Jigawa da Yobe da Sunshine FM Potiskum, duk suna da karfin da suke sauraransu sosai. A irin haka, a cikinsu a kan ji sunaye sababbi waxanda wasu iyaye ba ma kamar sababbin iyaye ba, su ari ire-iren waxannan sunaye su raxa wa 'ya'yansu.

Karance-karance na littattafan Hausa musamman na soyayya:

Wasu littattafai ana sanya su a yanar-gizo wato 'online', inda mutane za su iya buɗewa su karanta, baya ga karantawa na zahiri. Alal misali, littafi kamar na Hafsat A. (2001) – *So Aljannar duniya*. Ta wannan hanya ce sababbin iyaye suke amfani da ita wajen samun ire-iren sunayen da suke sanya wa 'ya'yansu sunan zamani. Akasari wannan kafa ta fi shafar wadànda suka yi karatun boko. Kodayake, wadànda ba su yi karantun boko ba, sukan yi aro a wurinsu. Wannan hanya ba ta da tasiri sosai idan aka kwatanta ta da sauran hanyoyin kamar yadda wasu suka nunar mani a lokacin da na yi hira ko tattauna da su.

Wasu Mutane masu xaukar ra'ayi:

Akwai wasu mutane masu xaukar sababbin abubuwa waxanda suke da ra'ayin cewa zamani riga ce in ya zo sai ka nema ka sa. Duk abin da ya zo in sun ga ya yi masu dadî ko abin da kowa da kowa ke yi, sai su yi. Wasu daga cikinsu kuwa, sun tafi a kan sun ga wane ya aikata ko ya sanya, shi ne su ma suka sanya.

Tafiye-tafiye:

Hausawa na masa kirari da "tafiya mabudîn ilmi". Wasu kuwa, na cewa "na zaune bai ga gari ba". Dogaro da wannan kirari, wasu ta wannan hanya ce suke samun nasu ire-iren sunayen, waxannan mutane matafiya ne waxanda da zarar sun dawo gida sai su sanya wa 'ya 'yansu sababbin sunayen aro.. Wannan ita ma wata babbar kafa ce da ake samun sababbin sunaye na zamani.

Sauraron Wa'azi:

Wannan ya shafi zuwa sauraron wa'azi na zahiri ko na talabijin ko na rediyo ko ta wayoyin hannu. Waxannan ba qananan kafafe ba ne ko hanyoyi da ke kawo sauyi a rayuwar Ɗan-adam ba. A nan, idan wani ya ji sunan wani daga cikin magabata kuma sunan ya yi masa daxi ta fuskar tarihi da gudumawar da ya bayar ga addinin Musulunci, sai shi ma ya aro ya radà wa ɗansa ko 'yarsa sunan. Wasu sunayen, kalmomi ne masu ma'ana, kamar Shukur, Ɗahira, Sabir ko Mahir ko Muhusin ko Anas da makamansu. Sannu a hankali, sai sunayen su yi tasiri a zukatansu, har ta kai ga radà wa yaro ko yarinya sunan.

Tattaunawa

A nan, tattaunawa za ta kasance ƙarkashin wadannan dalilai. Da farko akwai sanin muhimmancin suna: Wasu da aka yi hira da su, sun nunar da cewa, suna sanya sunan don sanin muhimmancinsa. Ma'ana sanin ma'anar sunan ko kalmar, mai kyau ce, tare da jin tarihin mai sunan da irin gudumawar da ya bayar wa al'umma ko addini. Misali Shukur wadda ke nufin godiya, ke nan, sai a kira yarinya da Shukura; Ɗahir na nufin mai tsarki, sai a kira yarinya da Ɗahira; Sabir na nufin haƙuri. Anas kuwa, sunan wani sahabi ne da ya tashi a gidan Manzon Allah (SAW) wanda yake da hali mai kyau da kuma bayar da gudumawa sosai ga addinin Musulunci wanda shi ne sabon-shiga iyaye idan suka ji sunan, sai suke raxa wa 'ya 'yansu da makamantansu.

Na biyu, Akwai takwara: Takwara na nufin sanya wa wani mutum mai suna. Akwai wasu da suke da ra'ayin sanya wa 'ya'yansu sunayen da manufar ya gaji mai sunan wajen kyauta ko haƙuri ko ilmi da sauransu. Sai dai, masu wannan ra'ayi sun kasance 'yan kadan, wasu kuwa, wannan ba shi ne manufarsu ba.

Haka kuma akwai al-kunya:

Alkunya kalma ce da ke nufin saye. Ma'ana kalma ce wadda ba a fitowa fili ɓaro-ɓaro a faxi sunan. A nan, sababbin iyaye ke amfani da wannan dama wajen sanya wa mahaifansu wato uwa da uba takwara. Idan yaro ne, sai a kira shi da sunan 'Walid,' idan kuma mace ce sai a kira ta da sunan 'Walida.' Sannu a hankali, wannan suna sai ya danne na yanka. Wasu kuma, sai a kan kira su da wani suna na alkunya. Misali. Idan sunan uwa Adama ce, a riqa kiranta da Shukura ko Mama ƙarama ko dai wani suna na daban. Haka zalika, idan namiji ne a kan kira shi da 'Walid' ko wani suna na daban. Saboda haka, sunan ke nan, har ta kai ga makaranta da lokacin aure. Kamar yadda sunan laqabi na rana ya yi tasiri, kamar irin su Ɗanladi ko Ɗanjuma, ko Ɗanjummai, ko Ɗanasabe, Laraba, ko Jummai da makamantansu, haka sunan zamani ke ƙoƙarin yin tasiri a yau.

Bincike ya nuna cewa, wani dalilin samuwar sunayen zamani shi ne ta hanyar ra'ayi, wasu sababbin iyaye suna sanya wa yaro ko yarinya suna a matsayin ra'ayi, domin ba su da wani dalili mai gamsarwa. Akasarinsu, dadîn sunan ne ya sanya suka raxa wa 'ya'yansu sunayen. Baya da haka, wasu daga cikinsu sun tafi a kan cewa sun ga wane ya sanya, shi ne su ma suka sanya. Wasu kuwa cewa suka yi zamani ne, don haka ba za a bar su a baya ba.

Kammalawa

Harshen Karai-Karai ya kasance ɗaya daga cikin harsunan Iyalan Chadi, sannan ɗaya daga cikin harsunan 'yan asalin Jihar Yobe. Za a same shi a Kudancin Yobe (Yobe South Senatorial District) inda suka yi makwabtaka da Ngizimawa da Bolewa da Ngamawa da Kanuri da Fulani. Daga cikin sunayen zamani, akwai Shukura da Muhibbat da Sabira da Sarad da Hafiza da Anas da Haidar da Khalifa da Mujahid da Ummi da Walida da Hamra da Walid da Khalil da Sabir da Barista da Anti da Momi da makamantansu,

Daga ƙarshe, wasu suna sanya sunayen sakamakon sanin ma'ana ko muhimmancinsa, wasu kuwa a matsayin alkunya wasu kuwa ra'ayi ne, Sannan, hanyoyin samuwar sunayen sun haɗa da kallace-kallacen na'urorin zamani da tafiye-tafiye da karance-karance da sauraron wa'azi da cuɗanya da wasu mutane da makamantansu.

Naxewa

A taqaice, wannan takarda ta bayyana kutsen zamananci wanda ya dabaibaye al'umma a yau shi ne raxin suna na zamani da sababbin shiga iyaye suke aro wanda ke qoqarin shafe sunan yanka. Sannan, hanyoyin samuwar waxannan sunayen sun haxa da kallace-kallacen wasu na'urorin zamani kamar talabijin da rediyo kana da tafiye-tafiye da karance-karance da sauraron wuraren wa'azi da sauransu. Manya dalilai da suka jawo sanya irin waxannan sunayen suna xamfare da sanin muhimmancin sunan da al'kunya kana da ra'ayi. Baya ga haka, sunayen sun haxa da Muhibbat da Walida da Ilham da Ummu Salma da Mufida da Hamra da Lawiza da Hafiza da Uzaifa da Hanif da Walid da Anas da Haidar da Khalifa da Anti da Barista da makamantansu. Duk waxannan sunaye da aka kawo da ma waxanda ba kawo ba, ba sunayen Karai-Karai ba ne na yanka, sun zo ne a bayan sunan yanka.

Sakamakon Bincike

Sananne ne cewa duk inda aka gudanar da wani bincike lallai a samu sakamakon. Saboda haka, wannan bincike ya gano akwai gagarumin tasiri da tasirintuwar sunan zamani a tsakanin sabbabin iyaye (maza da mata), musamman matasa waxanda shekarunsu ya fara daga ashirin da biyar zuwa hamsin (25-50) na sanya wa 'ya 'yansu suna ta hanyar aro. Irin waɗannan sunaye sun haɗa da Sukura da Sarad da Hanif da Khalifa da Haidar da Haifiza da Walid da Walida da Mufida da Ummi da Muhibbat da Anas da Sabir da sauransu da yawa. Har wa yau, bincike ya gano irin wannan al'ada ta aron sunaye babu birni babu ƙauye. A kowannensu suna gadar da wannan al'ada ta aron sababbin sunaye daga abubuwan da suka jivanci zamananci. Sanan, da yawa ba su damu da sanin ma'ana da tarihi ko gudumawar da mai irin sunan ya bai wa al'umma ko addini ba. Suna sanya sunaye bisa ra'ayi ko sha'awa.

Manazarta

Abubakar, A. (2001), *An Introductory Hausa Morphology*. Faculty of Arts. University of Maiduguri. Shafi. 30.

Abubakar, I. (2022), Tasirin Addini kan sunayen Karai-Karai na gargajiya cikin *Taguwa Journal of Humanities.* Vol. 11 No. I. June, 2022. Shafi. 231-237.

Abubakar I. (2018). "Tasirin Harshen Hausa a kan Harshen Ngizim a garin Potiskum na Jihar Yobe". Kundin Digiri na biyu, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Danfodiyo Sokoto.

Abdulwaheed, H. (2001), *So Aljannar Duniya*. Hamdan Press Nig. Limited. No.35 Army Road.

Ado, A. (2012). *Sunayen Hausawan Nijeriya da Misirawan Masar na Gargajiya a cikin tsarin abajadin Hausa*. www.darelhekma.net hassanelsharif@darelhekma.net Sh. 24-51.

Ado, A. (2019), *Ra'o'in Bincike kan al'adun Hausawa*. (Bugu na biyu), Government Printing Press. Nigeria. Sh. 89.

Babalala, M. (2022). Rahotan BBC Hausa na BBC Service. 26/12/2022. 08:45 pm.

Bunza, U. A. (2012),"Tasirin Zamani kan Sunayen Yanka na Diyan matan Hausawa: Tsokaci a taƙaice" cikin Munkaila, M.M. da Zulyadaini, B. (eds) *Language, Literature and Culture. Festschrift in Honour of Professor Abdulhamid Abubakar*. Department of Languages and Linguistics University of Maiduguri, Shafi. 651-659.

Danmaigoro, A. (2014)."Nazarin Ra'o'in da suka shafi al'adu da dangantakarsu ga al'adun Hausawa" *Himma Journal of Contemporary Hausa Studies*. Vol. 5 No. 1. Deparment of Nigerian Languages, Umaru Musa Yar'Adua University, Katsina.

Danmaigoro, A. (2010). "Sunayen Hausawa da Fulani" cikin Funtua, A. I da Gusau, S.M (eds) cikin *Al'aduda Dabi'un Hausawa da Fulani*. El-Abbas printers and media concepts No. 10 Gwari road. Sh. 158-168.

Gusau, S.M. (2015). *Mazhabobin Ra'I da Tarke a Adabi da Al'adu na Hausawa*. Century Research and Printing.

Greenberg, J.H. (1963), *The Languages of Africa. Bloomington.*

Greenberg J.H. (1966). *The Languages of African*. The Hague Mouton. P. 44-47.

Greenberg J.H. (1950). *Classification of African Languages Hermatic; Samiotic Southern Journal of Anthropology*. Pp 647.

Gwammaja, K.D. (2013). *Tsanin Hausa: Hausa Don Makarantun Firamare na 3.* Kamilu Gwammaja Bookshop Sabon Gari Market. Sh. 8-9.

Madauci, I. da Isah, Y. da Daura, B. (1982). *Hausa Customs*. Northern Nigerian Publishing Company Limited. Gaskiya Building. Sh. 6-9.

Newman, P. (1977), *Chadic Classification and Reconstruction*. *Afro-Asiatic Linguistics.* P. 77.

Sallau, B.A. (2011). Raxa Suna Jiya da Yau cikin Yalwa, L.D. da Baba, A.T. (ed) cikin *Himma Journal of Comtemporary Hausa Studies. Vol. 3*. Katsina. Department of Nigerian Languages, Umaru Musa Yar'adua University. Sh. 126-130.